Lallai Shaiɗan haƙiƙa ya yanke ƙaunar masu sallah su bauta masa a tsibirin larabawa, sai dai a sa gaba a tsakaninsu

Daga Jabir - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Na ji Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - yana cewa: "Lallai Shaiɗan haƙiƙa ya yanke ƙaunar masu sallah su bauta masa a tsibirin larabawa, sai dai a sa gaba a tsakaninsu".
[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa lallai Iblis ya yanke ƙaunar muminai masu sallah su dawo bautarsa da yi wa gunki sujjada a cikin tsibirin larabawa, sai dai cewa shi bai gusheba yana kwaɗayi, kuma bai gusheba ƙoƙarinsa da wahalarsa da tafiyarsa ba ta gushe ba a cusa rigingimu a zukatansu da gaba da yaƙe-yaƙe da fitintinu da makancin wannan a tsakaninsu.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/8886